**KOMAI NISAN JIFA III**

**EPISODE 10**

<u>Characters</u>

*Laraba*

*Eze*

*Tina*

*Hannah*

*Alhaji Bature*

*Safiya*

**Episode 10, Scene 1**

**Northern Kaduna. Eze's chemist shop. Early Afternoon**

1. **MUSIC:** **<u>THEME MUSIC</u>**
2. **SFX:** **<u>SOUND OF ROAD AMBIENCE WITH TRAFFIC NOISE. FOOTSTEP OF LARABA APPROACHING.</u>**
3. **LARABA:** **(UPBEAT)** Ah Mr. Eze, sannu da aiki! Ina yini?
4. **EZE:** **(COLDLY)** Na'am? Menene Nars Laraba**?**
5. **LARABA:** Toh Mr. Eze. Na zo ne game da maganan da muka yi akan kwamitin kiwon lafiya. Za'a fara mitin a sati me zuwa.
6. **EZE:** **(COLDLY)** Toh na ji.
7. **LARABA:** **(UPBEAT)** Ina fata zaka halarta kenan ko?
8. **EZE:** **(RUDELY)** Ban tsammani zan samu lokaci ma wannan kwamitin naki ba.
9. **LARABA:** **(SURPRISED)** A'ah! Mr. Eze, meyasa? Me ya faru?

10.**EZE:** **(OFFENSIVE)** Ke Nas Laraba, ina sane da duk abubuwan da kike ta fa*d*i akai na a wannan garin. Sai ki ringa dariya tare da ni, amma ki koma baya kina wata magana daban.

11.**LARABA:** **(UPSET)** Haba Mr. Eze! Wace irin magana ne wannan? Meyasa kake neman zagi na haka kawai?

**12.EZE:** **(CUTS IN)** Kar ma ki yi kamar baki san komai ba. Kina ganin kaman ban san yadda kike neman ki *b*ata mini bizines na a wannan garin abi?

**13.LARABA:** **(SHOCKED)** Ni?? Ta yaya?! Me na yi?

**14.EZE:** **(COLDLY)** Ke Nas Laraba, ni mutum ne me gaskiya, kuma ina kan aiki na. Ki dena yi mini tambayan da kin riga kin san amsa.

**15.LARABA:** Mr. Eze, na rantse ban san komai akan abun da kake fa*d*a ba!

16.**EZE:** Toh Nas Laraba, bari na gaya miki, na ji duk abubuwan da kika fa*d*a, harma da kika ce wai ni me bada maganin *k*arya ne, wai mutane su daina zuwa wuri na.

17.**LARABA:** *Haba* Mr. Eze! Ta yaya zan ce haka bayan kana cikin mutanen da na fara tuntu*b*a a wannan gari game da kwamitin. Ina girmama ka sosai, ban ta*b*a irin wannan magana ba a game da kai.

18.**EZE:** Toh! Kina son ki yi musu ko? Kina son ki ce baki yi wa Tanko fa*d*a ba domin ya zo wuri na?

19.**LARABA:** **(FRUSTRATED)** Aaah! Ba haka ya faru ba. Abun da na ce masa kawai shine …

**20.EZE:** **(CUTS IN ANGRILY)** Ban son na ji wata bayani. Na *d*auka kin ce baki ce komai ba? Toh wani bayani kike neman ki bada kuma?

21.**LARABA:** Abun da na gaya masa shine ya lura da irin magungunan da yake sha, ya kuma ringa neman shawaran masu aikin kiwon lafiya domin kar ya jawo wa kansa hallaka. Shi kenan.

**22.EZE:** Wato na zama mai kisa kenan ko? Ko kuma ina sayar da magunguna marasa kyau? Wannene a ciki Nas Laraba?

**23.LARABA:** **(APOLOGETICALLY)** Mr. Eze, baka gane ba. Ba haka bane. In ba komai ba, ka san cewa ina girmama ka da irin taimakon da kake yi a *b*angaren kiwon lafiyar wannan garin, kuma …

24.**EZE:** **(CUTS IN)** Nas Laraba, ko ma menene sunanki, bayaninki ya ishe ni, ki fita daga shago na kafin na ji haushi.

25.**LARABA:** **(AGITATED)** Gaskiya Eze, ba haka bane. Da zaka saurare ni …

26.**EZE:** **(CUTS IN, COLDLY)** Na ji kuma ya ishe ni, Nas Laraba don Allah ki tafi. Ai ko mai sayar da maganin *k*arya kaman ni baya son zama tare da masu munafirci.

27.**MUSIC:** **<u>BRIDGE MUSIC</u>**

**Episode 10, Scene 2**

**Southern Kaduna. Hannah and Danjuma's Residence. Late Afternoon.**

**28. MUSIC:** **<u>THEME MUSIC</u>**

**29. SFX:** **<u>ROOM AMBIENCE. SOUND OF DRAWER DOOR OPENS.</u>**

30.**HANNAH:** Tina, ban gane abun da kike cewa ba. Ki gaya mun dalilin da kike neman aron kayan sawa na?

31.**TINA:** Hmm Hannah, sai kin ga irin shigen da 'yan matan ofishin Yaya Danjuma ke yi.

32.**HANNAH:** Tina, ba zaki ha*d*a kanki da su ba! Su ma'aikata ne, ke kuma *d*aliba ce. Ba wanda zai yi tsammani zaki yi irin shigensu.

**33.TINA:** Ah! Ba haka bane fa a can. Sai nayi shige mai kyau idan ina son na daka ta nasu. Ko kayanki da nake nema ma basu kai nasu ba.

**34.HANNAH:** **(IRRITATED**) Amma ni ba ma'aikata bace ba. Meyasa zaki kwatanta kayana da nasu? Kuma ma wannan kamfanin gine-gine ne ba wata banki bane ko kuma wata ofishin shari'a. Me ya kawo wasu ha*dadd*un shige kuma?

**35.TINA:** Ah Hannah, zauna nan! Matan nan 'yan yayi ne! Jakakkunansu da takalmansu kawai na iya sayan duk kayan ki.

**36.HANNAH:** Toh Tina, gwara ki bar mun 'yan kayan arha na!

**37.TINA:** Ah Hannah, ba haka nake nufi ba. Ina so ne na zama daidai a wannan ofishin, saboda haka ya kamata na inganta salo na. **(TEASING)** Ko baki so nima na samu miji kaman Yaya Danjuma?

**38.HANNAH:** Tina, kar ki damu, komai da lokaci, zaki samu miji nagari ke ma. Ina miki addu'a.

**39.TINA:** Hannah, yanzu ne lokacin fa. Sai kin ga samarin dake ofishin.

40.**HANNAH:** Sai kuma ki shimfi*d*ar da kanki a gare su kawai ko? Ko kuma kin samu wani ne?

41.**TINA:** Eh, a ofishin. Yana da dattako, mai kiriki, yana *k*as*k*antar da kai, kuma mai ku*d*i!

42.**HANNAH:** **(SHOCKED)** Tina! Baki ma jin kunya... **(TEASING)** Har kin samo wa kanki naki "Danjuma" ko?

**43.TINA:** **(GIGGLING)** Shi kaman Yaya Danjuma ne.

44.**HANNAH:** Ina miki murna. Menene sunansa? Zan tambaye Danjuma ya bincika ko shi mutumin kirki ne.

45.**TINA:** **(UPSET)** Ahn a'a! don Allah kar ki gaya wa Yaya Danjuma. Zan ji kunya. Kuma shi mutumin na yi mini kallon 'yar uwar aiki ne kawai. Amma ina aiki akan sa.

46.**HANNAH:** Ah! Ki yi hankali fa. Ya kamata ki "Get it together", bana son ki shiga wata halin *k*in gani, ko kuma ki ji kunya.

**47.TINA:** **(PLAYFULY)** Ah! Haka ba zai faru ba.

**48.HANNAH:** **(SERIOUS)** Ba wasa nake ba fa Tina. Bana son ki zamanto uwa ba tare da aure ba, ko kuma ki zubar da ciki.

49.**TINA:** **(CURIOUS)** Amma ta yaya zan kare kai na daga irin wannan? Ba'a hana ka*dd*ara, ko ba haka ba?

50.**HANNAH:** Akwai hanyoyi dayawa masu amfani wajen kare kai daga shiga mumunan yanayin ba tare da wani shiri ba. Sai ki je asibiti domin neman *k*arin bayani.

51.**TINA:** Toh zan je. Amma Hannah, gaskiya kin ci sa'a da kika samu miji nagari, kuma kuna hul*d*arku a cikin soyayya.

52.**HANNAH:** **(SMILING)** Kar ki damu, kema zaki samu naki. Kar ki yi hanzari ki zo ki yi kuskure.

**53.TINA:** Hmm, Yaya Hannah, ba zai yi miki wuyan fa*d*an haka ba. Kina da Danjuman ki. Ba kowa ke da sa'a haka ba.

**54.MUSIC:** **BRIDGE MUSIC**

**Episode 10, Scene 3**

**Northern Kaduna. Alhaji Bature's Residence. Night.**

**55. SFX:** **SOUND OF BED CREAKING AS BATURE LIES DOWN.**

**56.SAFIYA:** **(GIGGLING)** Hmm, Alhaji kenan.

**57.BATURE:** Allah, ba wasa nake ba. Babu abun da zaki tambaye ni ban baki ba. Ko da kin ce na bar *k*asar ne. Ko ma menene.

**58.SAFIYA:** **(GIGGLING)** Hmm Alhaji Bature, ka tabbata?

**59.BATURE:** Safiya, amarya ta, na tabbata! Na ga cewa kuna da albarka a gidanku, kuna da ‘yan uwa maza dayawa, kuma ke ma kina da *d*a namiji. Na san zaki haifan mini yaro nima.

**60.SAFIYA:** Na gode mai gida. In sha Allah zan yi iya *k*o*k*ari na. Zaka cima burinka.

61.**BATURE:** Na yarda da haka. Kin san shiyasa na aure ki. Duk na saka rai akan ki, shiyasa zan yi miki duk abun da kike bu*k*ata.

**62.SAFIYA:** **(DISAPPOINTED, UPSET)** Alhaji Bature, kana nufin cewa shine dalilin da ka aure ni? Bayan kana ta yaba kyau na?

**63.BATURE:** **(SMILING)** Haba Safiya na! Kina da kyau mana. Amma ba shine babban dalilin da na aure ki ba.

**64.SAFIYA:** **(SADLY)** Wato dai ka aure ni ne domin na haifan maka yara? Bayan ma ina da niyyar yin tazzara tsakanin haihuwa da haihuwa saboda na samu *k*arfin jiki na iya kula da kai da yaran.

**65.BATURE:** Kalli nan Safiya, karmu wuce gaba, ki haifan mini *d*a namiji tukunna. Idan kin yi mun wannan zan baki duk abun da zaki iya bu*k*ata.

**66.MUSIC:** **<u>BRIDGE MUSIC</u>**

**Episode 10, Scene 4**

**Southern Kaduna. A boutique. Afternoon**

**67. MUSIC:** **<u>THEME MUSIC</u>**

**68. SFX:** **<u>SOUND OF NIGERIAN HIPHOP MUSIC PLAYING LOW VOLUME IN THE BACKGROUND</u>**

**69. SFX:** **<u>SOUND OF HANGERS MAKING NOISE ON A METAL RACK. SOUND OF HIGH HEELED FOOTSTEPS COMING ON MIC</u>**

**70.HANNAH:** Laraba, ya kika ga wannan rigar da siket. Zai yi mun? Na gaya miki wai shagon nan na da kaya masu kyau.

**71.LARABA:** Toh Hannah, ya *d*an bambanta daga kayan da kika saba sa wa. Baki ganin yayi bau dayawa?

**72.HANNAH:** Laraba, na sayo wasu mujalla kuma irin wa*d*annan kayan ne ake yayi. Ana kiran su 'toshe-kala'.

**73.LARABA:** **(LAUGHING)** Hannah, wato zaki iya ha*d*a kalolin nan tare?

**74.HANNAH:** **(LAUGHING)** Kina da gaskiya Laraba. Danjuma zai ce na haukace idan ya gan ni na ha*d*a irin kalolin nan.

**75.LARABA:** **(LAUGHING HARDER)** Kuma shi mutum ne mai sau*k*in kai, ina tunanin yadda zai ajiye fuska idan …

**76.HANNAH:** Kowa na zato wai Danjuma shiru-shiru ne, da kin gan shi lokacin da gaya masa wai na *d*auki juna biyu**.**

**77.LARABA:** **(SURPRISED)** Juna biyu! Da gaske Hannah? Kai! Ina miki murna.

**78.HANNAH:** **(HAPPY)** Na gode!

**79.LARABA:** **(CONFUSED)** Toh ai ya kamata mu saya irin kayan masu juna biyu ko? Ko kuma yadi ki *d*inka dogayen riguna. Domin Hannah, nan da *d*an watanni kayan nan baza su shige ki ba.

**80.HANNAH:** **(DISAGREES)** A'a. Laraba ya kamata na saya kaya masu kyau, musamman irin kayan da ake yayi saboda**…**

**81.LARABA:** Saboda me Hannah? *K*awata, ki gaya mun mana, salon yayi bai ta*b*a damunki ba.

82.**HANNAH:** Laraba, 'yar uwata Tina ta gaya mun wai matan dake aiki a ofishin Danjuma na saka kaya masu kyau sosai. Saboda haka ya kamata nima na ringa yin shige mai kyau a duk lokaci.

83.**LARABA**: **(SMILING)** Hannah, ba sai kin yi wata gasa dasu ba. Ko baki yarda da maigidanki ba. Kin san yana *k*aunar ki, ba zai kalli wasu matan ba.

84.**HANNAH:** Hmmm Laraba, baki kallon fina-finai ne? Akwai matan da zasu yi iyakan *k*o*k*arinsu su anshe miki miji.

**85.LARABA:** **(LAUGHS)** Hannah, manta da wannan. Kin san irin mijin da kike dashi. Ya kamata ki yarda dashi.

**86.HANNAH:** Kina da gaskiya Laraba. Na yarda da Danjuma. **(DISMISSING)** Na gaji da batu na, me ke faruwa dake ne? Kina ta sabawa da garinmu ko?

87.**LARABA:** Ina jin da*d*in aikin, kuma na gode da cewa babu wanda ya san tarihi na. Ina iya kwantadda hankali na.

**88.HANNAH:** Mun gode wa Allah. Shine amfani canza yanayi. Za'a samu kwanciyar hankali.

89.**LARABA:** Ha*k*i*k*a. **(WORRIED)** Amma ina tsoron cewa rashin sa'a na ya biyo ni.

**90.HANNAH:** Ta yaya? Ban gane ba**.**

91.**LARABA:** **(SADLY)** Na samu *d*an damuwa tare da sirkan uwar *d*aki na, sai kuma tare da Eze mai sayar da magani. Ina ganin cewa sun san da rashin sa'a na shiyasa yawancinsu basu so na.

92.**HANNAH:** Ban tsammani rashin sa'a ne ya jawo wannan.

**93.LARABA:** **(LAUGHS BITTERLY)** Hmmm Hannah, idan ba rashin sa'a bane to ai da damuwa kenan. Kenan akwai wani abu game da ni wanda ke sa mutane su *k*i ni.

94.**HANNAH:** Laraba, wannan ba shi bane! Kar ki dame kanki. Mutane biyu ne kawai a cikin duk mutanen Kaduna da kika samu damuwa tare dasu.

**95.LARABA:** **(TEASING)** Amma ina ganin Tanko me kayan koli ma baya so na. Mutane uku kenan ba biyu ba.

**96.HANNAH:** **(LAUGHING)** Laraba kin cika bada dariya. Toh mutane uku a wannan garin basu son ki, kar ki damu, domin basu san ki bane. Da zaran sun san ki zasu so ki.

97.**LARABA:** Toh Hannah, ina sa rai haka ne. Sabon yayani a Kaduna ya kamata ya kawo *k*arshen rashin sa'a a rayuwa ta.

98.**MUSIC:** <u>**BRIDGE MUSIC**</u>